Ya Manzon Allah, lallai Ummu Sa'ad ta rasu, to wace sadaka ce tafi?. Ya ce: "Ruwa". Ya ce: Sai ya haƙa wata rijiya, ya ce: Wannan ga Ummu Sa'ad ce

Daga Sa'ad ɗan Ubada - Allah Ya yarda da shi - cewa shi ya ce: Ya Manzon Allah, lallai Ummu Sa'ad ta rasu, to wace sadaka ce tafi?. Ya ce: "Ruwa". Ya ce: Sai ya haƙa wata rijiya, ya ce: Wannan ga Ummu Sa'ad ce.

[Hasan ne ta jimillar hanyoyinsa] [Abu Dawud da Nasa'i da ibn Majah ne Suka Rawaito shi]

Mahaifiyar Sa'ad ɗan Ubada - Allah Ya yarda da shi - ta rasu, sai ya tambayi Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - game da mafificin nau'ikan sadaka dan ya yi sadaka dashi ga mahaifiyarsa? sai tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya ba shi labarin: Cewa mafificiyar sadaka ita ce ruwa, sai ya haƙa wata rijiya ya sanyata sadaka ga mahaifiyarsa.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/65613